


# Me ka sani game da Dabarun Tazarar Haihuwa?

| DABARU/HANYOYI | CIKKAKEN BAYANI | LOKUTAN INGA-NCIN SU |
|---|---|---|
| **KWAYOYIN MAGANIN TAZARAR HAIHUWA NA SHA**  | • Ingantancen kwayoyin tazara wanda ake shan kwaya daya a kowace rana<br>• Ba su da hadari ga mata komin shekarun su ko matan da ba su taba haihuwa ba<br>• Ba su da hadari ga mace mai shayarwa | Gajeren lokaci |
| **ALLURAR**  | • Ingantacen hanyar tazarar haihuwa ta gajeren lokaci cikin wata biyu ko uku<br>• Ba su da hadari ga mata komin shekarun su ko matan da ba su taba haihuwa ba<br>• Ba su da hadari ga mace mai shayar da jaririn da ya dare sati shida | Gajeren lokaci |
| **ASHANAN FATA MAI SINADARI**  | • Ingantaciyar hanyar tazarar haihuwa ta dogon lokuta cikin shekaru uku zuwa biyar<br>• Ba su da hadari ga mata komin shekarun su ko matan da ba su taba haihuwa ba<br>• Ba su da hadari ga mata masu shayarwa | Dogon Lokaci |
| **ROBAR MAHAIFA**  | • Ingantacen hanyar tazarar haihuwa ta dogon lokuta cikin shekaru biyar zuwa goma<br>• Ba su da hadari ga mata komin shekarun su ko matan da ba su taba haihuwa ba<br>• Ba su da hadari ga mata masu shayarwa<br>Ana iya saka robar mahaifa a lokacin da mace ta haihu (bayan fitowar mabiya zuwa kwana biyu 48 hour) ko bayan sati 4 na farko bayan haihuwa | Dogon Lokaci |
| **KWORORON ROBAR MAZA**  | • Ingantacen hanyar tazarar haihuwa ta gajeren lokaci wanda ake amfani da shi a lokacin jima'i<br>• Da zaran an bi dokokin amfani da kwororon roba, za ta bada:<br>- Kariya da ga daukar ciki<br>- Kariya daga kamuwa da cututtukan sanyi da kwayar sida | Gajeren lokaci |
| **KWORORON ROBAR MATA**  | • Ingantacen hanyar tazarar haihuwa ta gajeren lokaci wanda ake amfani da shi a lokacin jima'i<br>• Da zaran an bi dokokin amfani da kwororon roba, za ta bada:<br>- Kariya da ga daukar ciki<br>- Kariya daga kamuwa da cututtukan sanyi da kwayar sida<br>• Babu hadari ga mata masu shayarwa | Gajeren lokaci |
| **SHAYAR DA NONON UWA ZALLA-LAM**  | • Hanya ce mai inganci idan mace ta tsare wadannan ka'idoji guda uku:<br>- Mace tana shayar da jaririn nono zalla (dare da rana) ba tare da bayar da ruwa ko wani abinci ba<br>- Mace tana da jariri kasa da wata shida da haihuwa<br>- Idan bata ga jinin al ada ba tun bayan haihuwa | Gajeren lokaci |
| **DAURE MAHAIFA**  | • Ingantacen hanyar tazara na mata masu bukatan tsayar da, ko kuma daina haihuwa | Na Dindindin |
| **JUYAN MAZAKUTA**  | • Ingantacen hanyar tazara na maza masu bukatan daina, ko kuma tsayar da haihuwa | Na Dindindin |

© NURHI 2017

**TUNTUBI JAMI'AN ASIBITI KAN DABARU TAZARAN HAIHUWA**

Get it together
KNOW. TALK. GO.

NURHI 2
NIGERIAN URBAN REPRODUCTIVE HEALTH INITIATIVE